# Ƙwayar cutar Ebola



## ME CE ITA?


- Kwayar cuta ke haifar da Ebola.
- Zuwa yanzu babu allura, kuma babu magani na wannan cuta – **AMMA neman magani DA WURI a Cibiyoyin Lura da Cutar Ebola na iya taimakawa wajen warkewa**
- Ta na haifar da rashin lafiya mai tsanani tare da zubar jinni
- Tana da saurin yaɗuwa; za ta iya kama mutane da yawa
- Zuwa kashi chasa'in daga cikin dari zasu mutu





## TA YAYA TA KE BAZUWA?

- Marasa lafiya na iya baza cutar ga sauran jama'a
- Mutanen da suka yi hulɗa da masu cutar sun fi zama cikin haɗari:
  - Dangin mara lafiya
  - Ma'aikatan jiyya



Matattu na iya yaɗa cutar. A LURA. (A binne cikin lura. A kau da jiki)

- KA DA a wanke, taɓa ko kuma sumbantar mamaci
- KA DA a wanke hannu a bokiti guda da wanda ya taɓa mamaci

## ALAMOMIN

Kan iya faraway kwanaki 2-21 daga lokacin da aka yi hulɗa da mai cutar ko jikinsa

### ALAMOMIN KAMUWA

### ALAMOMIN DA ZA SU BIYO BAYA



ZAZZAƁI



TASHIN ZUCIYA



CIWON KAI



GAJIYA



AMAI

Zai iya haɗawa da jini



GUDAWA

Zai iya haɗawa da jini



TARI


Zai iya haɗawa da jini



ZUBAR JINI

(daga hanci, baki, fata)

## KARIYA



- ZA KA IYA KAMUWA DA EBOLA DAGA WANDA KE DA CUTAR KO MAMACI
- WANKE HANNUNKU AKAI-AKAI – Yi amfani da SABULU (Idan ba'a sami damar wankewa ba ayi amfani da man wanke hannu)




- Ka da ka taɓa wanda ya kamu ko ruwan da ya fita daga jikinsa JINI, AMAI, BAYAN-GARI KO GUDAWA, FITSARI
- Akwai EBOLA a jikin dabbobi da jemagu. KA DA a taɓa ko kuma cin "naman farauta" ko jemagu

## ME ZA KA YI idan ka sami rashin lafiya



- Kirawo asibitinku kuma ka shaida musu yanayin cutar
- Saurari shawararsu.
- Za'a iya turaka asibiti na musamman
- Rabu da sauran mutane sabo da kada su kamu
- Yi hankali da amanka da kuma gudawa




**Koda ya ke babu maganin cutar, neman magani DA WURI a Cibiyoyin Lura da Cutar Ebola na iya taimakawa wajen warkewa.**

Wannan bayani an yi shi ne domin faɗakarwa kawai, kuma ya dace da lokacin da aka wallafa shi. Bai zama madadin shawarar ƙwararre a kan harkar lafiya ba. Idan akwai wata tambaya ko damuwa a kan abin da aka ambata, a hanzarta a tuntuɓi ƙwararre kan harkar lafiya.

© 2014 AEA International Holdings Pte. Ltd. All rights reserved. Unauthorised copy or distribution prohibited.

25 August 2014 HAUSA

TRANSLATORS WITHOUT BORDERS

International SOS™